# Kara Bibiyar Salon *Iƙtibasi* a *Waƙar Bidi'a* ta Malam Sa'adu Zungur

Jibril Shu'aibu Adamu, Ph.D
Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya,
Jami'ar Bayero, Kano
+2348069441480
jsadamu.hau@buk.edu.ng

**Tsakure**

Wannan takarda ta ƙunshi bayanin yadda Malam Sa'du Zungur ya sarrafa nassi a cikin *Waƙar Bidi'a*. Manufar takardar ita ce ƙara bibiyar nassi da fito da shi a cikin *Waƙar Bidi'a* biyo bayan binciken Mainasara (2018). A wajen gudanar wannan takarda an ƙara nazartar *Waƙar Bidi'a* kamar yadda ta zo a cikin Abdulƙadir (1974) da kuma Yakubu (1999). Haka nan an ɗora wannan takarda a kan hanyar nazarin nassi kamar yadda masana suka kawo. Wannan takarda ta yi nasarar gano ƙarin wasu nassoshi da aka yi amfani da su a cikin *Waƙar Bidi'a* ƙari ga waɗanda Mainasara (2018) ya gano. Dangane da tsakuren nassi guda uku (3) da aka gano a binciken Mainasara (2018), wannan takarda ta kuma gano ƙarin baitoci uku masu ƙunshe da tsakuren nassi. Dangane da fassarar nassi guda huɗu (4) da Mainasara (2018) ya gano, wannan takarda ta kuma gano ƙarin guda uku (3). Game da abin da ya shafi ishara zuwa ga nassi, wannan takarda ta kuma gano ƙarin misali ɗaya ƙari ga na Mainasara (2018) guda uku (3).

***Muhimman kalmomi:*** Sa'adu Zungur, *Waƙar Bidi'a*, Nassi, Tsakuren Nassi, Fassarar Nassi, Ishara ga Nassi.

## 1.0 Gabatarwa

Malam Sa'adu Zungur, wato Ahmed Mahmud Sa'adu Zungur ya kasance malamin addinin Musulunci, ɗan boko, ɗan kishin ƙasa, ɗan siyasa kuma marubucin waƙoƙi wanda ya rayu a cikin ƙarni na ashirin kuma ya bayar da gagarumar gudummuwa wajen cigaban ƙasar Nijeriya. Malam Sa'adu Zungur ya rubuta waƙoƙi da dama, *Waƙar Bidi'a* ɗaya ce daga cikin waƙoƙinsa wanda niyyar wannan takarda shi ne ta yi nazarinta. Masana da manazarta sun gudanar da ayyuka da dama a kan rayuwa da ayyukan Malam Sa'adu Zungur. Wasu ayyukan kamar su Kano (1973) da Yakubu (1999) duk sun kawo tarihin Sa'adu Zungur a yalwace. Haka nan ayyuka irin su Zungur (1968) da Abdulƙadir (1974) sun kawo wasu waƙoƙin Sa'adu Zungur, domin Abdulƙadir (1974) ma har nazarin wasu muhimman waƙoƙin Zungur ya yi guda huɗu, ciki kuwa har da wannan waƙa da wannan takarda ta mayar da hankali a kanta, wato *Waƙar Bidi'a*. Kazalika Murtala (2013) ya yi nazarin *Waƙar Bidi'a* ta mahangar addinin Musulunci, a yayin da Mainasara (2018) ya yi nazarin amfani da salon *Iƙtibasi*, wato amfani nassoshin Alƙur'ani da Hadisai a *Waƙar Bidi'a'*. Laila Usman Shehu (2019) ta yi nazarin aruli ne na waƙar *Arewa Jamhuriya ko Mulukiya* ta hanyar amfani da Ra'i mai nasaba da Tsarin Sauti. Adamu (2025) kuwa ya yi nazarin kayan yaƙin Hausawa ne na gargajiya a cikin *Waƙar Yaƙi da Shaiɗani* da Sa'adu Zungur. Feiyang da Nura (2025) sun yi nazarin *Waƙar Arewa, Jamhuriya ko Mulukiya*?.Yakubu (2026) kuwa nazarin waƙar Sa'adu Zungur ne ta ƙarshe ya yi, wato *Waƙar Jihadin Neman Sawaba*.

Bisa la'akari da waɗannan ayyuka da aka yi a kan rayuwa da waƙoƙin Malam Sa'adu Zungur kamar yadda aka kawo wasu a sama, za a ga masana da manazarta sun yi bincike da nazarce-nazarce a kan waƙoƙin Sa'adu Zungur, musamman ma *Waƙar Bidi'a* wadda Murtala (2013) da Mainasara (2018) suka gudanar da nazari a kanta. Duk da cewa binciken Mainsara (2018) yana da nasaba kai tsaye da wannan takarda, kasancewar shi ma ya yi nazarin iƙtibasi a *Waƙar Bidi'a*, sai dai ba duka nassoshi aka fito da su aka yi bayaninsu a cikin nazarin ba. Saboda haka manufar wanann takarda ita ce ƙara bibiyar *Waƙar Bidi'a* domin fito da nassoshin da Mainasara (2018) bai yi bayaninsu a nazarin waƙar ba. An samo matanin *Waƙar Bidi'a* a Abdulƙadir (1974) da kuma Yakubu (1999). Haka kuma an yi amfani da *Alƙur'ani*, mai girma da kuma littattafan Hadisai domin gano da ƙara fito da nassoshin da aka kawo a cikin wannan waƙa.

## 2.0 Wane ne Sa'adu Zungur?

Sa'adu Zungur kamar yadda aka bayyana a baya, ya kasance malamin addinin Musulunci ɗan boko, ɗan siyasa ɗan kishin ƙasa kuma marubucin waƙoƙi. An haife shi a shekarar 1915 a Gundumar Galadima, wani gari mai kimanin nisan mil ashirin da biyar (25) daga garin Bauchi (Abdulƙadir, 1974:9)[1]. Kasancewar Sa'adu Zungur an haife shi a gidan malamai, wannan ya ba shi damar karatun addinin Muslunci a wajen mahaifinsa Malam Muhammadu Bello. Zungur ya karanci fiƙihu da tauhidi da nahawun Larabci da Alƙur'ani da kuma tafsirin Alƙur'ani a wajen mahaifinsa. Bayan nan mahaifin Sa'adu ya saka shi a Makarantar Lardi ta Bauchi a shekarar 1922, sannan daga nan a shekarar 1926 Sa'adu ya halarci Kwalejin Katsina. Daga shekarar 1929 zuwa 1934 ya halarci Kwalejin Yaba da ke Ikko[2]. Bayan kammala karatu ne a Kwalejin Yaba Zungur ya sa sami aikin koyarwa a Makarantar Malaman Tsafta ta Zariya a shekarar 1936 inda a wannan makaranta ne ya kafa wata ƙungiya mai suna *Zaria Literary Society* a shekarar 1939. Kazalika ya sake kafa wata ƙungiya mai suna *Zaria Improvement Union* a shekarar 1941. A shekarar 1947 ne ya kafa ƙungiyar *The Youth Social Circle*. Haka kuma a shekarar 1951 ne ya shiga jam'iyyar *Northern Peoples Congress* (NPC) da kuma *National Council of Nigeria and Cameroons* (NCNC) a shekarar 1948. A shekarar 1950 ya shiga *Northern Elements Progressive Union* (NEPU) ya kuma fice daga NCNC a shekarar 1952. Haka nan ya jagoranci reshen NEPU na Jihar Bauchi bayan shekarar 1953 (Abdulƙadir, 1974, sh. 9)[3].

Dangane da rubuta waƙa kuwa, *WaƙarYaƙi da Shaiɗani* ita ce waƙar Malam Sa'adu Zungur ta farko da ya rubuta yana ɗan shekara ashirin (20) kafin ko jim kaɗan bayan ya bar Kwalejin Yaba da ke Ikko (Yakubu, 1999, sh. 25). Amma zuwa tsakiyar ƙarni na goma sha tara, Malam Sa'adu Zungur ya zamanto shi ne ja-gaban marubuta waƙoƙi a Arewacin Nijeriya a zamaninsu. Kuma waƙoƙinsa sun yi matuƙar tasiri a wajen al'umma kasancewar jigoginsu a kan batutuwa ne da suke faruwa a wannan lokaci. Ta kai saboda matuƙar shaharar waƙoƙinsa yara 'yan makaranta suna hardace da rera waƙoƙinsa (Abdulƙadir, 1974, sh. 8). Wasu daga cikin shahararrun waƙoƙin da Malam Sa'adu Zungur ya rubuta sun haɗa da *Waƙar Bidi'a* (wadda aka nazarta a cikin wannan takarda) da *Waƙar Maraba da Soja* da *Waƙar 'Yan Baka* da *Waƙar Arewa Jumhuriya ko Mulukiya*? da *Waƙar Mulkin Nasara* da *Waƙar Yaƙi da Shaiɗani* da kuma *Waƙar Jihadin Neman Sawaba* (Abdulƙadir, 1974, sh. 5 da Yakubu, 1999, sh. 292-397).

---

[1] Yakubu (1999, sh. 8) cewa ya yi a shekarar 1914 aka haifi Malam Sa'adu Zungur a Mazaɓar Ganjuwa ta Kwaryar Birnin Bauchi.

[2] Abdulƙadir (1974, sh. 10) ya bayyana cewa Malam Sa'adu Zungur ne mutum ɗan Arewacin Nijeriya na farko da ya fara samun gurbin karatu a Kwalejin Yaba da ke Ikko.

[3] Domin ƙarin bayani dangane da tarihi da gwagwarmayar rayuwar Malam Sa'adu Zungur a duba Kano (1973) da Abdulƙadir (1974) da kuma Yakubu (1999).

Allahu Akbar! Allah ya ɗauki rayuwar Malam Sa'adu Zungur bayan doguwar jinya da ya sha fama da ita a shekarar 1958 yana ɗan shekara arba'in da biyar.

## 3.0 Salsalar *Waƙar Bidi'a*

An samo wannan *Waƙar Bidi'a* ne a cikin Zungur (1968, sh. 1-6), da Abdulƙadir (1974, sh. 16-30), da kuma Yakubu (1999, sh. 320-335), kuma wannan waƙa tana da baitoci tamanin da biyar (84) kamar yadda aka kawo ta a cikin waɗannan ayyuka da aka ambata a baya. Jigon wannan waƙa shi ne yaƙi da bidi'a[4], wato abin da aka ƙirƙiro rana tsaka a cikin addinin (CNHN, 2006, sh.45). Haka zalika, ita wannan waƙa an tsara ta ne cikin ɗango bibbiyu, wato waƙar ƙwar biyu ce, sannan kuma babban amsa-amonta, wato ƙafiya shi ne 'a' inda kowane baiti na waƙar yake ƙarewa da shi. Dangane da aruli kuwa, an tsara wannan waƙa ne a kan Karin Basit (Abdulƙadir, 1974: sh. 35).

## 4.0 Salon *Iƙtibasi* a *Waƙar Bidi'a*

*Iƙtibasi*, kalma ce ta Larabci da take ɗaukar ma'anar kafa hujja daga Alƙur'ani mai girma da kuma Hadisi, musamman a cikin rubutu. Wannan salo shi ne manazarta adabin Hausa suke kira da Salon Sarrafa Nassi (Birnin-Tudu, 2013), ko Luguden Nassi (Bunza, 2009) ko Sarrafa Nassin Alƙur'ani (Omar Sa'adiya, 2013).

A ƙarƙashin wannan galibi akan duba abubuwan irin su: (i) Gundarin Nassi, wato inda aka ambaci nassin Larabci kai tsaye a cikin rubutu, da (ii) Fassarar Nassi, wato inda ake kawo fassarar nassin Larabci cikin harshen Hausa, da kuma (iii) Ishara Zuwa ga Nassi, wato a nan nuni ake yi zuwa ga nassi. Ga bayanansu kamar yadda aka ƙara fito da su a cikin *Waƙar Bidi'a* kamar haka:

### 4.1 Kara Bibiyar Tsakuren (Gundarin) Nassi a *Waƙar Bidi'a*

Tsakuren nassi yana nufin a ɗauko wani sashe na nassi don kafa hujja, wato a ɗebo wani yanki na ayar *Alƙur'ani* mai girma ko Hadisi (Birnin-Tudu, 2013:166). Idan aka duba Mainasara (2018) an ga inda ya fito da baitoci kimanin guda uku (3) waɗanda suke ƙunshe da gundarin nassi cikin harshen Larabci. Wani abin da ya kamata a lura da shi a wannan takarda shi ne, ba za a sake bibiyar sharhin baitocin da Mainasara (2018) ya kawo ba, sai dai kawai a kawo baitocin. Ga gundarin nassin Larabci da ya kawo a cikin *Waƙar Bidi'a* kamar haka:

1. Ka ɗaura aniya a kan waƙa kana addu'a,
   ***A'uzu Billah*** daga Shaiɗani a kan bidi'a.

7. Manzo ya ce ***la tazalu*** tutur akwai jama'a,
   Da za ta dage a kan sunna da ƙin bidi'a.

78. ***Subhana Rabbika Rabbil'izzati amma,***
   ***Yasifuna***, domin rashin ilimi ga 'yan bidi'a.
   (Mainasara, 2018, sh. 148).

Idan aka kalli waɗannan baitoci kamar yadda suka gabata, kamar yadda aka kaurara su da kuma yi musu alamar tafiyar-tsutsa, za a ga baitoci ne da suke ɗauke da abin da ake kira

[4] Don ƙarin bayani a kan Kalmar bidi'a, a duba Murtala (2013).

gundarin nassin Larabci da suka zo a Alƙur'ani mai tsarki, da kuma Hadisan Manzon Allah mai tsira da aminci. Domin ƙrin bayani sai a duba Mainasara (2018, sh. 148).

Wasu tsakuren gundarin nassin Larabci da wannan takarda ta ƙara fito da su a cikin wannan waƙa mai suna *Waƙar Bidi'a* su ne kamar haka:

Misali na 1:

41. ***Fa'in tawallau***, idan suka soma bauɗewa,
    Suka juya baya ga ma'anar kamilar ɗa'a.

Idan aka kalli wannan misali na 1 da ya zo a baiti na 41 na *Waƙar Bidi'a*, za a ga yana ƙunshe da tsakuren nassin Larabci, wato ***Fa'in tawallau*** wanda yake tsakure ne daga farkon Ayar Alƙur'ani mai girma da ta zo a cikin Sura ta Tara (9), wato *Surah At-tawbah* [Surar Tuba], Aya ta 129. Ga cikakkiyar Ayar kamar yadda ta zo a cikin *Suratu At-Tauba* kamar haka:

﴿فَإِن تَوَلَّوْا۟ فَقُلْ حَسْبِىَ ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ۖ عَلَيْهِ تَوَكَّلْتُ ۖ وَهُوَ رَبُّ ٱلْعَرْشِ ٱلْعَظِيمِ﴾

Idan aka duba duba farkon Ayar inda ka ja wa layi a ƙarƙashi, za a ga gundarin tsakuren nassin kamar yadda Malam Sa'adu Zungur ya kawo shi a cikin baiti na 41 a waƙarsa mai suna *Waƙar Bidi'a* kamar yadda aka gani a baya. Ga kuma fassarar Ayar cikin harshen Hausa kamar haka:

> *"To idan sun ba da baya sai ka ce "Allah Ya ishe ni, babu wani abin bautawa da gaskiya sai Shi, a gare Shi kaɗai na dogara; kuma Shi ne Ubangijin Al'arshi mai girma.*" (Rijiyar Lemo, 2021, Mujalladi na Biyu (1), sh. 608).

Wani misali na tsakuren nassin Alƙur'ani da aka ƙara bibiya da kuma fito da shi a cikin *Waƙar Bidi'a* ta Malam Sa'adu Zungur an gano su ne a baitoci na 42 da kuma na 43. Ga baitocin tafe kamar haka:

Misali na 2:

42. Su je da niyyarsu mu dai ***hasbunal-lahu,***
    ***Wani'ima***, madalla mai tanyon dukkan jama'a.

43. ***Ni'imal Wakilu*** mu dogara gunsa ba tsaro,
    ***Ni'iman Nasiru*** bisa kan taimakon jama'a.

Idan aka duba misali na 2 da ya gabata mai ɗauke da baiti na 42, a nan ma an ga a ɗango na farko da kuma na biyu, mawallafin *Waƙar Bidi'a*, wato Malam Sa'adu Zungur, ya kawo tsakuren gundarin nassin Alƙur'ani mai tsarki, wato ***hasbunal-lahu***, da kuma ***wani'ma*** waɗannda duka ya tsakuro su ne daga a Aya ta 173, *Suratu Ali Imran*. Haka nan idan aka duba baiti na 43 na *Waƙar Bidi'a*, za a ga mawallafin ya kawo tsakuren ƙarshen Aya ta 173 ta *Suratu Ali Imran.* Ga gundarin Ayar kamar yadda ya zo a surar kamar haka:

﴿ٱلَّذِينَ قَالَ لَهُمُ ٱلنَّاسُ إِنَّ ٱلنَّاسَ قَدۡ جَمَعُواْ لَكُمۡ فَٱخۡشَوۡهُمۡ فَزَادَهُمۡ إِيمَٰنٗا وَقَالُواْ <u>حَسۡبُنَا ٱللَّهُ وَنِعۡمَ ٱلۡوَكِيلُ</u>﴾

Ga fassarar Aya ta 173 da aka yiwo tsakaurenta a cikin a *Suratu Ali Imran* kamar haka cikin harshen Hausa:

> *"Su ne waɗanda mutane suka ce da su : "Lalle mutanen (Makka) fa sun tara muku runduna, to sai ku tsorace su. "Amma sai hakan ya ƙara musu imani, sai suka riƙa cewa : "Allah Ya wadace mu, kuma madalla da abin dogaro (idan har Shi ne Allah).*", (Rijiyar Lemo, 2021, Mujalladi na Ɗaya (1), sh. 493).

Kazalika, idan aka duba ɗango na biyu na baiti na 43 da Malam Sa'adu Zungur ya kawo a *Waƙar Bidi'a,* za a tarar tsakuren ƙarshen Aya ta 40 ne cikin *Suratu Anfal.* Ga gundarin Ayar kamar yadda ya zo a cikin Surar kamar haka:

﴿وَإِن تَوَلَّوۡاْ فَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَوۡلَىٰكُمۡۚ نِعۡمَ ٱلۡمَوۡلَىٰ <u>وَنِعۡمَ ٱلنَّصِيرُ</u>﴾

Ga fassarar Ayar ta 80 da aka yiwo tsakurenta a cikin a *Suratu Anfal* kamar haka cikin harshen Hausa:

> "*Idan kuma suka ba da baya, to ka sani cewa, Allah (Shi ne) Majiɓici, kuma madalla da wannan Mai taimako*" (Rijiyar Lemo, 2021, Majalladi na Biyu (2), sh. 444).

Har wa yau, a ci gaba da ƙara bibiyar nassi a cikin *Waƙar Bidi'a* ta Malam Sa'adu Zungur, an kuma cin karo da wani baiti wanda yake ɗauke da tsakuren nassin Alƙur'ani mai girma wanda ba a ambace shi a cikin Mainasara (2018) ba. Ga tsakuren nassin Alƙur'anin kamar yadda ya bayyan a baiti na 44 na waƙar kamar haka:

Misali na 3:

44. ***Iyyaka na'abudu*** bauta wada ba shirka,
    ***Iyyaka*** kuma ***nasta'inu*** a kan gudun bidi'a.

A wannan misali da ya gabata, Zungur ya kawo tsakuren Aya ta 5 cikin *Suratul Fatiha*, wato Sura ta farko a cikin *Alƙur'ani* mai girma, wato "***Iyyaka na'abudu***" a cikin ɗango na farko da kuma '***iyyaka nas'tainu*** a ɗango na biyun baitin. An yi tsakuren ne da fassara daga Ayar da take cewa watau Allah kaɗai muka yarda mu bauta wa; dukkan nau'o'in ibada gare shi ake ba da su. Ibada kuwa ita ce, duk wani abu da Allah yake son sa kuma ya yarda da shi, na ƙuduri ne a zuciya ko magana ta baka ko kuma aiki na gaɓoɓi. Sannan mun tabbata ba za mu iya bauta masa yadda ya dace ba sai da taimakonsa. Don haka a wajensa kaɗai muke neman taimako a cikin lamurranmu gaba ɗaya. Wannan yana nuna ba a neman taimakon wani wanda ba Allah ba a duk wani abu da Allah ne kaɗai zai iya yin sa, kamar bayar da arziki ko neman lafiya, ko neman 'ya'ya da makamantansu. Bai halatta wani ya kira wani annabi ko wani waliyyi ko wani salihin bawa ba yayin da yake cikin wata musiba don ya taimake shi, idan har ya yi haka to ya bayar da

haƙƙin Allah ga wani, watau ya yi shirka da Allah (Rijiyar Lemo, 2020, 7). Ga gundarin Ayar da aka yo tsakuren nata kamar haka:

﴿إِيَّاكَ نَعْبُدُ وَإِيَّاكَ نَسْتَعِينُ٥﴾

Ga fassarar Ayar cikin harshen Hausa kamar haka:

*Kai kaɗai muke bauta wa, kuma Kai kaɗai muke neman taimakonka.*
(Rijiyar Lemo, 2021, Mujalladi na Ɗaya (1), sh. 34).

**4.2 Kara Fito da Fassarar Nassi a *Waƙar Bidi'a***

A misalan da suka gabata, an ƙara fito da gundarin nassi ne a cikin *Waƙar Bidi'a*. Misalan da suke tafe a nan kuwa, sun shafi fassarar nassi ne, wanda yake nufin ciro fassarar wata aya ta *Alƙur'ani*, mai girma ko Hadisi (Birnin-Tudu, 2013:164). Mainasara (2018) ya kawo fassarar nassi kamar yadda suka zo a cikin baitoci huɗu (4) na *Waƙar Bidi'a*, wato baiti na uku (3) da na tara (9) da na goma (10) da na arba'in da shida (46). Gai baitocin nan tafe kamar yadda suka zo a cikin *Waƙar Bidi'a*.

3. Daɗa kawo salsala don kammalar ɗa'a,
Ga wanda aikensa rahama ce wajen jama'a.

9. Allah ya yi umarni duk ga al'umma,
A kan riƙon igiyarsa da tattalin jama'a.

10. Kuma kar a rarraba don koyi da al'ummai,
Da sunka saba umarni suka bar ɗa'a.

46. Hanyar waɗannan da kai ni'ima gare su duka,
Ai banda hanyar miyagu tarkacen bidi'a.
(Mainasara, 2018, sh. 148-150)

A wannan takarda an ƙara bibiya da kuma fito da wasu wurare da aka sami fassarar nassi na Hadisai da kuma na Alƙur'ani a cikin *Waƙar Bidi'a*. Baitocin da aka ƙara ganowa suna ɗauke da nassi su ne baiti na 12 da baiti na 13 da kuma baiti na 47 kamar yadda za a ga bayaninsu tafe:

A baiti na 12 da na 13 na *Waƙar Bidi'a*, wannan takarda ta gano Malam Sa'adu Zungur ya kawo fassarar wani Hadisi ne da yake maganar al'ummar Ma'aiki za ta rabu zuwa gida har saba'in da uku, wadda a cikin wannan kashi ɗaya ne zai tsira. Ga baitin kamar haka kamar yadda ya zo a cikin *Waƙar Bidi'a*:

Misali na 4:

12. Da ya ce a kwana a tashi sannu za mu rabu,
Saba'in da ukku tafirka duk muna bidi'a.
**13. Face guda ɗaya ita ce za ta san tsira,**
**Sauran a tura Jahannama don rashin ɗa'a.**

Idan aka duba waɗannan baitoci guda biyu, wato baiti na 12 da na 13 kamar yadda suka zo a *Waƙar Bidi'a*, za a ga ci gaba da fassarar Hadisi ne mai lamba 3992 wanda ya zo a cikin Sunan Ibn Majah. Ga fassarar Hadisin a taƙaice kamar haka:

> "Yahudawa sun rabu gida 71, Nasara sun rabu gida 72, kuma al'ummata za ta rabu gida 73; dukansu a Wuta sai guda ɗaya." Sai aka tambaye shi: "Wace ce wannan guda ɗaya, Ya Manzon Allah?" Sai ya ce: "Wadda take kan abin da ni da Sahabbaina muke a kai (*Sunan Ibn Majah*, #3992, *Sunan at-Tirmidhi*, # 2641).

Kazalika, a cikin *Waƙar Bidi'a* ta Malam Sa'adu Zungur, an kuma bibiya da gano baiti na 47 na waƙar wanda yake ɗauke da fassarar Aya ta 7 ce ta *Suratu Fatiha* kamar haka:

Misali na 5:

47. Bayin da ka yi hushi bisa kansu don saɓo,
    Da waɗanda sunka ɓace don shirku kan ɗa'a.

Ga Ayar da aka fassara ta cikin wannan baiti kamar haka:

﴿صِرَٰطَ ٱلَّذِينَ أَنۡعَمۡتَ عَلَيۡهِمۡ غَيۡرِ ٱلۡمَغۡضُوبِ عَلَيۡهِمۡ وَلَا ٱلضَّآلِّينَ﴾

Ga fassarar Ayar cikin harshen Hausa kamar haka:

"*Tafarkin waɗanda Ka yi wa ni'ima, ba waɗanda ka yi fushi da su ba, ba kuma ɓatattu ba"* (Rijiyar Lemo, 2021, Mujalladi na Ɗaya (1), sh. 36).

### 4.3 Kara Fito da Ishara Zuwa ga Nassi a *Waƙar Bidi'a*

Baya ga fassarar nassi kamar yadda aka gani a misalan da suka gabata, a nan za a mayar da hankali ne a kan ishara zuwa ga nassi, wanda yake nufin nuni ga nassi ba kai tsaye ba. A nan za a yi bayani ne wanda zai nuna wata aya ce aka taɓo. Mainsara (2018, sh. 150-151) ya kawo misali na baitocin *Waƙar Bidi'a* da suke nuni ko ishara zuwa ga nassi. Baitocin da ya nazarta sun haɗa da baiti na talatin da biyar (35) da na talatin da takwas (38) da kuma na hamsin da ɗaya (51) kamar haka :

35. Su ce dukan iliminka na za shi kai ushirin,
    Na ubanka ko malaminka, a zamanin bidi'a.

38. To, ɗan'uwa sai ka jure kuma ka ɗau haƙuri,
    Bisa gargaɗin jama'ammu su daina yin bidi'a.

51. In taimako ne ka ke nema a kan lamari,
    Sai dai ka tsarkake niyyar ka ta yin addu'a.

(Mainasara, 2018, sh. 150-151)

Baya ga waɗannan misalai na ishara zuwa ga nassi da Mainasara (2018) ya kawo a cikin takardarsa, wannan takarda ta sake gano baiti na 65 a cikin *Waƙar Bidi'a* ta Malam Sa'adu Zungur, wanda yake ishara ga Hadisin Ma'aiki wanda yake hana rantsuwa da wanin Allah. Ga baitin kamar yadda ya zo a cikin waƙar:

Misali na 6:

65. Daɗai ba ka ji shi ya rantse da Allah ba,
    Don ƙarfafawar batunsa don yana bidi'a.

Kamar yadda aka ambata a baya, wannan ishara da Hadisi wanda ya zo a cikin Sunan Abi Dauda, Hadisi na 3242. Ga fassarar Hadisin a taƙaice kamar haka:

> *Manzon Allah ya ce: "Kada ku yi rantsuwa da sunayen iyayenku (maza), ko iyayenku (mata), ko waɗanda ake ɗauka tamkar kishiyoyin Allah; ku yi rantsuwa da Allah kaɗai, kuma ku yi rantsuwa da Allah ne kawai idan kuna faɗin gaskiya.*" (Sunan Abi Dawud 3248).[5]

Baya ga wannan Hadisi, akwai Hadisai da dama da suke hani da rantsuwa da wanin Allah waɗanda za a iya cewa baiti na 65 na Waƙar Bidi'a yana nuni gare su.

## 6. Kammalawa

**Alhamdulillahi,** a nan ne aka kawo ƙarshen wannan takarda wadda tun daga farkonta aka buɗe ta da kawo taƙaitaccen tarihin Malam Sa'adu Zungur wanda shi ya wallafa *Waƙar Bidi'a*. Haka nan an kawo taƙaitaccen bayani game da salsalar waƙar. Har ila yau, an ɗan bibiyi ma'anar salon amfani da nassi.

Bayan kammala wannan takarda, an gano *Waƙar Bidi'a* tana ɗauke wasu nassoshi ƙari ga waɗanda Mainasara (2018) ya gano. Dangane da tsakuren gundarin nassi, wannan takarda ta kuma fito ƙarin misalai a baitoci na 41, da na 42, da na 43 da kuma na 44, wato ƙari ga baitoci na 1 da na 2 da kuma na 78 da Mainsara (2028) ya gano. Haka nan dangane da abin da ya shafi fassarar nassi, wannan takarda ta ƙara gano misali a baiti na 12 da na 13 da kuma na 47, waɗanda suke ƙari ne ga baitoci na 3 da 9 da na 10 da kuma na 46 da Mainasara (2018) ya gano. Daga ƙarshe wannan takarda ta kuma gano wani ƙarin misali da yake ishara da Hadisi, wato baiti na 65, wanda yake ƙari ne ga baitoci na 35 da na 38 da kuma na 51 da Mainsara (2018) ya gano. Wani muhimmin abin da ya kamata a lura da shi, shi ne wannan bincike ba shi ne ƙarshe ba dangane da *Waƙar Bidi'a*, ta yiwu idan aka ƙara zurfafa bincike a kuma gano wasu nassoshi da Malam Sa'adu Zungur a cikin waƙar ƙari ga waɗannan da aka riga aka fito da su.

## Manazarta


Abdulƙadir, Ɗ. (1974). *The Poetry, Life and Opinion of Sa'adu Zungur*. Zaria: NNPC.

Adamu, J. S. (2019). 'Amfani da Nassi a Wasu Waƙoƙin (Dr.) Mamman Shata Katsina'. in Aliyu Mu'azu, Isa Mukhtar, Hafizu Miko Yakasai, Tijjani Shehu Almajir, Muhammad Sulaiman


[5] Wannan fassarar mawallafin wannan takarda ne.

Abdullahi & Nura Lawal (Eds.) *Conference Proceedings on Alhaji (Dr.) Mamman Shata in Honour Dr. Aliyu Modibbo Umar [Danmburan Gombe]*, pp. 799-806.

Adamu, J. S. (2023). 'Sarrafa Nassi a Wasu Waqoqin Narambaxa' in Aliyu Mu'azu, Isa Mukhtar, Tijjani Shehu Almajir, Muhammad Sulaiman Abdullahi & Nura Lawal (Eds.) *International Conference on Ibrahim Narambaɗa Tubali in Honour of His Excellency, General Ibrahim Badamasi Babangida (rtd), GCFR*, pp.105-112.

Adamu, J. S. (2023). Ɗanƙwairo da Addini: Bibiyar Nassi a Wasu Waƙoƙin Musa Ɗanƙwairo', in Sa'idu Muhammad Gusau, Ahmad Magaji, Ibrahim Garba Satatima, Isa Yusuf Chamo & Muhammad Ammani (Eds.), *Studies on the Poetic Dynasty of Musa Ɗanƙwairo Mai Turu Ƙaen Makaɗa Kurna Maradun: Proceedings of the 30th Years of Commemorative Conference on Musa Ɗanƙwairo Maradun*, pp.501-510.

Adamu, J. S. (2025). 'Bibiyar Wasu Kayan Yaƙin Hausawa na Gargajiya a *Waƙar Yaƙi da Shaiɗani* ta Sa'adu Zungur'. in *Rumfa: Journal of Arts, Vol*. 4, No. 1, pp.135-147.

Adamu, J.S. (2017). Traces of the Arabic Literary Traditions in Modern Hausa Ajami Poetry

Birnin-Tudu, S. Y. (2013). *Jigo da Salon Rubutattun Waƙoƙin Furu'a na Karni na Ashirin.* Iqra'a Publishing House.

Birniwa, H.A (1987) "Conservatism and Dissent: A Comparative Study of NPC/NPN and NEPU/PRP Hausa Political Verse from Circa 1946 to 1983". Unpublished Ph.D Thesis, Department of Nigerian Languages, University of Sokoto, Sokoto.

Bunza, A. M. (2009). *Narambaɗa.* Ibrish Islamic Publication Centre Limited.

CNHN (2006) *Kamusun Hausa.* Zaria: Ahmadu Bello University Press.
*Discourse*.Vol.5. No.4. Pp.176-183.

Feiyang, L. da Lawal, N. (2025). 'Tunanin Siyasa a *Waƙar Arewa, Jamhuriya ko Mulukiya*'. in *Algaita: Journal of Current Research in Hausa Studies*, Vol. 18, No. 1, pp.230-244.

Gaya, A. S. (1972) "*Comparison Between Mu'azu Haɗeja and Sa'adu Zungur*". B. A. Dissertation, A.B.U/B.U.K.

Hiskett, M. (1075). The Development of Sa'adu Zungur's Political Thought from Maraba da Sooja, through Arewa Jumhuuriyya Koo Muluukiyaa, to Wakar Yancii. African Language Studies.XVI, pp.1-23.

Ingawa, S. Y. (2014) "Concluding Marɓyn Hiskett's Thesis on Sa'adu Zungur's Waƙar 'Yanci". Muƙalar da aka samu a shafin Sa'adu Zungur na yanar gizo. https://www.academia.edu/24471231/CONCLUDING_MERƊYN_HISKETTS_THESIS_ON_SAADU_ZUNGURS_WAKAR_YANCI.

Jabbi, U. and Yahaya I. (2018). Is Democracy Liberationist? The Gospel According to Late Malam Sa'adu Zungur. *Scholars Journal of Arts, Humanities and Social Sciences*, Vol.6. No.12. Pp. 2256-2262.

Kano, A. (1973) *Rayuwar Ahmad Mahmud Sa'adu Zungur.* Zaria.
Liberation of Northern Political System. *International Journal of Intellectual*

Mainasara, A. (2018). 'Nazarin Salon *Iƙtibasi* a Cikin "Waƙar Bidi'a" Ta Malam Sa'adu Zungur'. In *ALSUN Journal of Humanities*, Maiden Edition, Al-qalam University, Katsina, pp.146-151.

Malumfashi, I. A. M. (2012) "Who was Sa'adu Zungur? A Literary Historian's Glimpse". Takardar da aka gabatar a taron ƙara wa juna ilimi karo na bakwai kan matsayin adabi a Arewacin Nijeriya, wanda Jami'ar Bayero, Kano tare da haɗin guiwar Jami'ar Jihar Kwara, Malete suka shirya.

Muhammad, I. S. (2018). Nigeria's Uncelebrated Hero, Poet, Progressive Politician, Intellectual and Nationalist: Ahmad Mahmud Sa'adu Zungur' in *Journal of humanities and Cultures Studies* R&D, Vol.3, No.3, pp.

Murtala, A. (2013). 'The Illusion of Innovators: An Appraisal of Malam Sa'adu Zungur's Poem Against Bid'ah. In *Algaita: Journal of Current Research in Hausa Studies*, Vol. 1, No. 7, pp. 85-115.

Omar, Sa'adiya (2013). *Fasahar Mazan Jiya: Nazari a kan Rayuwa da Waƙoƙin Malam Mu'azu Haɗeja*. Garkuwa Media Services Limited.

Rijiyar Lemo, S. U. (2020). *Fayyataccen Bayani na Ma'anoni da Shiriyar Alƙur'ani* (1-6). Bayyinat Centre for Qur'anic Studies.

Shehu, U. L. (2019). 'Prosodic Analysis of Sa'adu Zungur's Poem Arewa Jamhuriya ko Mulukiya Using Phonological Approach'. Unpublished B.A. Dissertation, Department of Nigerian Languages, Bayero University, Kano.
Unpublished PhD Thesis, University of Warsaw, Poland.

Usman, U. L. (2024). *Sa'adu Zungur: Taƙaitaccen Tarihin Haɗuwarmu da shi da kuma Gwagwarmayar Siyasar NEPU a Bauchi*. Bauchi: Family of Alhaji Launi.

Yahaya, M. and Musa A. (2022). Analysis of Malam Sa'adu Zungur Political Thoughts on

Yakubu, A. M. (1999). *Sa'adu Zungur: A Anthology of the Social and Political Writings of a Nigerian Nationalist*. Nigerian Defense Academy Press.

Yakubu, A. M. (2026). *Sa'adu Zungur's Last Verse*. Arewa House: Ahmadu Bello University, Zaria.

Yusuf, J. (2016). 'Alƙalami Ya Fi Takobi: Nazarin Kaifin Alƙalamin Malam Sa'adu Zungur a Fagen Dagar Siyasar Nijeriya'. Maƙalar da aka gabatar a taron ƙara wa juna sani na Ƙasa da Ƙasa na Biyu Kan 'Heroes and Heroines of Hausaland' da Sashen Koyar Da Harsunan Nijeriya da Ilimin Kimiyyar Harsuna, Jami'ar Jihar Kaduna ta shirya, a ranakun 3-5 ga watan Yuni, 2016.

Zungur, S. (1968) *Waƙoƙin Sa'adu Zungur*. N.N.P.C Zaria.

## Rataye: Matanin *Waƙar Bidi'a*[6] ta Malam Sa'adu Zungur

1. Ka ɗaura aniya a kan waƙa kana addu'a,
   ***A'uzu Billah*** daga Shaiɗani a kan bidi'a.
2. San nan kawo Bamala bisa kan riƙon sunna,
   Ka biya da yin Hamdala ita ce uwar sa'a.
3. **Daɗa kawo salsala don kammalar ɗa'a,**
   **Ga wanda aikensa rahama ce wajen jama'a.**
4. Ka iyar da kalar Salatu zuwa ga Alaye,
   Da sallama ga Sahabbai masu kyan ɗa'a.
5. Da tabi'ina da Tabi'ihim sa ihsani,
   A kan tafarki na sunna wanda ba bidi'a.
6. Da malaman gaskiya fitilu na zamani,
   Don haskakawar duhun fitinu na mai bidi'a.
7. Manzo ya ce ***la tazalu*** tutur akwai jama'a,
   Da za ta dage a kan sunna da ƙin bidi'a.
8. Da waɗanda kuma za su juya kan dugagensu,
   Domin su koma ga arnanci na son bidi'a.
9. **Allah ya yi umarni duk ga al'umma,**
   **A kan riƙon igiyarsa da tattalin jama'a.**
10. **Kuma kar a rarraba don koyi da al'ummai,**
    **Da sunka saba umarni suka bar ɗa'a.**
11. Yau ga shi mun saɓa juna mun zamo bamban,
    Bisa kan Hadisi na Manzo Annabin sa'a.
12. Da yace a kwana a tashi sannu za mu rabu,
    Saba'in da ukku tafirka duk muna bidi'a.
13. Face guda ɗaya ita ce za ta san tsira,
    Sauran a tura Jahannama don rashin ɗa'a.
14. Allah Ta'ala muna roƙonka taufiƙi,
    Ka fid da mu rundunar jama'a ta 'yan bidi'a.
15. Ya ɗan'uwana da ke fatawa a kan zancen,
    Tawakkali da du'a'i wadda ba bidi'a.
16. Da fassarar ƙaddara wadda ba bidi'a,
    Cikin kitabu da sunna inda ba bidi'a.
17. A kan bayani na malamai da sunka faɗi,
    Domin ka gane tafarki wanda ba bidi'a.
18. Ai ka yi fatawarka gun wannan da bai da sani,
    Kuma bai da hikima ta rarrabe mas'alar bidi'a.
19. Sai rungume ni mu faɗi, ko kuwa ta Sakwaf,
    Da Lakwaf ya ce ya yi sai ka daina ba'a.

[6] An samo matanin wannan waƙar ne a cikin Abdulƙadir (1974) da kuma Yakubu (1999).

20. Sakwaf ya ce bai sakewa don gazawarsa,
    In ya sake ya faɗi, abin kamar da ba'a.
21. Ko kumburin wani ciwo ɗan'uwa ya gani,
    A gare mu yai tuhuma ta ƙiba da kyan dara'a.
22. Kuma dai ala kulli halin na ji fatawarka,
    Bisa tsarkakarka ga niyya kan gudun bidi'a.
23. Saura ka saurari amsa wadda za ta fito,
    Daga gun faƙihai na malaman cikin jama'a.
24. Amma abokin jawabin naka bai da batu,
    Na kansa sai wasiɗanci kam batum jama'a.
25. Allah ya shirye mu mu duka mui riƙon sunna,
    Mu kama igiya ta taufiƙi a kan ɗa'a.
26. Idan jawabinmu ya dace da fatawarka,
    Kai Hamdala kuma ka zage tattalin jama'a.
27. Ka jure suka ta kibiyoyi na jahilai,
    Don za su harbe ka, ka zarge su a kan bidi'a.
28. Ina sunka cije a kan zarginka ce, "Allah",
    San nan kabar su cikin ruɗinsu 'yan bidi'a.
29. Farko sukan ce karambaninka zai ja ka,
    Zuwa ga halakarka don ka zargi 'yan bidi'a.
30. San nan su juya tambayoyi na ɓata mutum,
    Har ma su kafirta al'amarinka kan bidi'a.
31. Su ce da kai zindiƙi don rashin taƙawa,
    Don ka yi suka ga al'ada ta 'yan bidi'a.
32. Ko ko su far ma da sunaye na malammai,
    Gagga da sunka ƙi yin wa'azi a bar bidi'a.
33. Ko kuma a ce garin nan ɗan su wane ne,
    Ya ke shigam manahanci kan batun bidi'a.
34. Ai ko ubansa a zamanin da ya yi,
    Yana ganinmu da girma kan batun bidi'a.
35. Su ce dukan iliminka na za shi kai ushirin,
    Na ubanka ko malaminka, a zamanin bidi'a.
36. Su ce dukkan lamarin nan nasu yai asali,
    Tun kan iyaye da kakanni a ke bidi'a.
37. Saura ku bar shi cikin haukansa har ya gama,
    Samartaka da rashin kunya ta 'yan sa'a.
38. To, ɗan'uwa sai ka jure kuma ka ɗau haƙuri,
    Bisa gargaɗin jama'ammu su daina yin bidi'a.
39. Dukan masibar da ta auku wa addini,
    Tushenta koyi da kakannin mutan bidi'a.
40. Duba ga nassi kan zan koyi da Manzanni,
    A kan jidali da al'adu na 'yan bidi'a.
41. ***Fa'in tawallau***, idan suka soma bauɗewa,

Suka juya baya ga ma'anar kamilar ɗa'a.

**42.** Su je da niyyarsu mu dai ***hasbunal-lahu,***
***Wani'ima***, madalla mai tanyon dukkan jama'a.

**43.** ***Ni'imal Wakilu*** mu dogara gunsa ba tsaro,
***Ni'iman Nasiru*** bisa kan taimakon jama'a.

44. ***Iyyaka na'abudu*** bauta wada ba shirka,
***Iyyaka*** kuma ***nasta'inu*** a kan gudun bidi'a.

45. Ya Rabbi shirye mu hanya wadda babu kwana,
Hanya ta bayin da suka san kamilar ɗa'a.

**46. Hanyar waɗannan da kai ni'ima gare su duka,**
**Ai banda hanyar miyagu tarkacen bidi'a.**

47. Bayin da ka yi hushi bisa kansu don saɓo,
Da waɗanda sunka ɓace don shirku kan ɗa'a.

48. Amina, ya Rabbi amsawarka mun ka biɗa,
Domin mu san ni'ima bisa dawwamar sa'a.

49. Ya ɗan'uwa mai biɗar tanyo wurin Allah,
Don tattalin gaskiya haƙƙin dubun jama'a.

50. Zamma nasiyya ka daina zuwa wurin tsafi,
Da Majalisar malaman duba da mai ƙuri'a.

51. In taimako ne ka ke nema a kan lamari,
Sai dai ka tsarkake niyyar ka ta yin addu'a.

52. Ai babul ale da Arabiyya wurin Allah,
Im babu ilmi na nahawu gare ka ko raf'a.

53. Ka wo kirari da harshen nan da kai ka iya,
Matuƙar akwai ihlasi babu ko bidi'a.

54. Sharaɗin du'a'I da Arabiyya yana da wuya,
Lallai ka san fassara tasa gwargwadon wus'a.

55. Im ba sanin fassara zancenka duk sururu,
Ya zam hululun da ba roƙo ba, ba addu'a.

56. Im ba sanin ma'ana kuma babu ihlasi,
Kuma ya zamo ba huluri ya zamo bidi'a.

57. Labudda ko wace doka ai ta kan togas,
A nan fa sai Alƙur'ani wanda bai da sa'a.

58. Sharaɗinsa ai ɗaya ne in dai akwai lafazi,
Mai kyau akwai li'irabi sai ya zam addu'a.

59. Sai dai gal ada ƙira'a ai da fifiko,
Ga mai sanin ma'ana don kammalar addu'a.

60. Amma fa sauran du'a'i ko na wane ne,
Tilas a san ma'anarsa a kauce yin bidi'a.

61. Ai hasali kai du'a'i duk da hausarka,
Im ba sanin Arabiyya gwargwadon wus'a.

62. Shi dai du'a'i sharuɗɗan nasa na da wuya,
Tilas mu yarfar da al'adun mutan bidi'a.

63. Da sannu dai za mu komo kan batun sharaɗi,
    Na yin du'a'I bisa zancen da babu ba'a.
64. Ga wani jawabi da yai suka ga al'ada,
    Ta rantsuwar jahili don ƙarfafar bidi'a.
65. Daɗai ba ka ji shi ya rantse da Allah ba,
    Don ƙarfafawar batunsa don yana bidi'a.
66. Sai dai ya rantse da hubbare na kakansa,
    Ko ko da tsohon ubansa a Majalisar bidi'a.
67. Kamar ya rantse da Ahmadu Shehu Tijjani,
    Ko Shehu Jailani, wai a zatonsa yai ɗa'a.
68. Ko ko aradu kwarankwatsa tabbatar tsafi,
    Bisa rantsuwarsu ta Arna zamanin bidi'a.
69. Kuma Shehu ɗan Hodiyonmu da shi da Hubbare,
    Suna cikin rantsuwar magana ta 'yan bidi'a.
70. In ko abin ya yi zurfi har ya je matuƙa,
    Domin a ƙarfada zancen Majalisar bidi'a.
71. Sai kuma a rantse da Annabi ko da Alƙur'ani,
    Da Mala'ikun Rahamanu a Majalisar bidi'a.
72. Kai hasali duk Bahaushe jahili tsantsa,
    Da furfurarsa ya kan rantse a kan bidi'a.
73. In ka ji ya ce da kai Wallahi ƙarya ce,
    Ya ɗungumata yana tuhumarka ko da ba'a.
74. Ko ko yana dariya zance na wargi ne,
    Ko kuma ya gunce Billahil-lazi da ba'a.
75. Wai don akwai rangwame bisa rantsuwar wargi,
    Allahu ba ya riƙo bisa rantsuwar dafa'a.
76. Da dai a ce da Bahaushe in ya je shari'a,
    Ya yi rantsuwarsa da Shehunnai a kan bidi'a.
77. Zai gwammace iƙirari ko mukulli don,
    A zuciyarsa da can gun Majalisar bidi'a.
**78.** ***Subhana Rabbika Rabbil'izzati amma,***
    ***Yasifuna***, domin rashin ilimi ga 'yan bidi'a.
79. Kar duba nassin Risala ƙirawaniyya,
    A kan batun rantsuwa domin ka bar bidi'a.
80. Mai son ya rantse idan dais hi Musulmi ne,
    Kuma mumuni mai basira mai yawan ɗa'a.
81. Sai dai ya rantse da Allah ko ya daina duk,
    Bisa ƙa'idar Musulunci wadda ba bidi'a.
82. Na san akwai wasu turaye na jihilai,
    Da za su dage ga al'adu ta bin bidi'a.
83. Su dinga yawon farauta inda malamai,
    Suna biɗar ta'awulin rantsuwar bidi'a.

84. Allah Ta'ala muna roƙo ka shirye su,
Su kama igiya ta Allah duk su bar bidi'a.
(Abdulƙadir, 1974, sh. 16-30)